RABON GADO

[TAKAITACCIYAR HANYA 2]

IBRAHIM SULEIMAN GWARAM

AFRILU 2024 / RAMADAN 1446 AH]

[RABON GADO is a book on Inheritance in Islamic jurisprudence written in Hausa language spoken in Nigeria.The book explains how wealth left behind by a deceased in a family is shared among his living children, parents and other relatives. It lays much emphasis on the practical aspect of sharing the wealth unlike other books written on the same subject whose emphasis were more on theoretical aspects.Tables and charts were shown at the end of every topic treated summarizing its content.Finally the book has been proof read by great Scholars and was found useful for readers interested in the field, especially those who understand Hausa language]

RABON GADO:

TAKAITACCIYAR HANYA

LITTAFI NA BIYU (2)

IBRAHIM SULEIMAN GWARAM

ISBN: 978-56973-7-7

RAMADAN, 1446 AH

AFRILU, 2024

ABUBUWAN DA KE CIKI

Sadaukarwa…….

Godiya…….

Gabatarwa……...

BABI NA: SHAFI NA:

1. Hukuncin Rabon Gadon da ya shafi Munasakha ……...1
   a. Halaye uku na Rabon Munasakha ……....1
   b. Yadda ake gudanar da Rabon Munasakha ……...3
2. Fita daga cin Gado (*Attakharuj*) ……..14
3. Rabon Gado ga Zul-Arham 16
   a. Sharrudan cin Gadon Zul-Arham ……....18
   b. Yadda ake rabawa Zul-Arham dukiyar Gado ……..19
4. Rabon Gado tare da Magaji Mata-maza (*Al-Khunsa*) ……23
   a. Tantance Mata-maza a matsayin Namiji ko Mace ……23
   b. Dangantakar Mata-maza da Mamaci ……....24
   c. Yadda ake raba Gado tare da Mata-maza (*Malikiyya*) ……24
   d. Yadda ake raba Gado tare da Mata-maza (*Shafi'iyya*) …..29
5. Rabon Gado tare da Dan-ciki (*Al-ham-lu*) ……...35
   a. Sharrudan bayar da Gado ga Dan-ciki 36
   b. Dangantakar Dan-ciki da Mamaci …….37
   c. Yadda ake raba Gado tare da Dan-ciki ……..……38
6. Rabon Gado tare da wanda ya `bace (*Al-maf-kud*) …...……...42
   a. Yadda ake tantance halin wanda ya `bace ……42
   b. Yadda ake raba Gado tare da Al-maf-kud 44
7. Gadon Magada juna wadanda su ka mutu tare ……47

   Amsoshin tambayoyi ……...…50

   Litattafan da aka duba ……55

SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan littafi ga mahaifiyata, Marigayiya Malama Khadija Idris, Gwaram, a Jihar Jigawa. Allah ya yi mata rahama, amin.

GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya sanar da mutum abinda bai sani ba. Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu (SAW) da alayensa da sahabbansa gaba dayansu.

Bayan haka ina matukar godiya ga sarkin malaman Jahun, Malam Hamza Umar wanda ya bada shawarwari wajen tsara littafin kuma ya dauki dawainiyar gyara shi kalma bayan kalma. Sai kuma Yusuf Alkhasim na "Yusuf Computers International, Birnin kudu", wanda ya dauki hakuri kwarai da gaske wajen tsara littafin a computer.

Ina godiya ga Malaman da suka duba littafin kuma suka sanya albarka, kamar Ustaz Haruna Hashim Gumel, Khadi Bashir Jahun, da Mujahid Malam Bayero Adamu, Jigawar Sarki,karamar hukumar Dutse. Sai mashahuran Malamanmu na Kano kamar su Dr. Umar Sani Fage da Sheikh Aminu Ibrahim Daurawa.

Ina kara godiya ga duk wadanda suka taimaka wajen bugawa da kaddamarwar wannan littafi, musamman masarautar Dutse,a karkashin jagorancin Mai martaba Sarkin Dutse Alh. Dr. Muhammadu Nuhu Sunusi. Allah ya kara masa lafiya tare da Imani.

A ƙarshe ba zan manta da ɗalibata ba, mai albarka, marubuciya Jamila Umar Tanko bisa jajircewarta wajen ƙarawa littafin farin-jini da ƙarɓuwa a wajen jama'a

Na gode.

JAWABIN MALAMINA AKAN LITTAFIN

Bismillahir Rahmanir Rahim

Godiya ta tabbata ga Allah madaukaki, wanda ya yiwa musulmi wasiya akan gado. Tsira da amincin Allah su tabbata ga manzo Muhammad (S.A.W), wanda ya ce “ku koyi ilmin rabon gado, kuma ku koyawa mutane domin shine rabin ilmi, kuma shine farkon ilmin da za’a manta a cikin al’ummata”.

Bayan haka na duba wannan littafi wanda yake dan karami amma kuma babba ne idan ka duba irin abubuwan da ya kunsa da kuma yawan fa’idarsa. Na tabbata idan mai karatu ya daure ya bishi a hankali, hakika, zai amfana da abubuwa masu yawa wanda zai yi wuya samun irinsu a tace kamar yadda suke anan.

Mafiya yawan littattafan da ake wallafawa sunfi bada muhimmanci ne akan ilmin rabon gado akarance ba a aikace ba. Wannan littafin ya bada kokari kwarai da gaske wajen fitar da mas’alolin gado a’aikace wanda na tabbata zai amfani mutane wajen koyon rabon gado ta wannan takaitacciyar hanya.

Da fatan Allah ya karbi wannan aiki ya sanya shi mai albarka kuma ya sanya shi cikin mizanin aiyukan malamin na alkhairi, da kuma dai duk sauran mutanen da suka taimaka littafin ya tabbata, amin.

M. Hamza Umar Jahun

Sarkin Malamai Jahun

Lakcara a Kwalejin Ilmi, Gumel

SANYA ALBARKA

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah mai rayawa da kashewa. Shine ya wajabta raba gado tsakanin maza da mata, yara da manya.

Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu masoyinmu kuma annabinmu Muhammad dan Abdullahi, bawan Allah kuma manzonsa tare da mutanen gidansa da sahabbansa gaba dayansu.

Babu shakka wannan littafi mai suna “Rabon Gado: Takaitacciyar hanya” wanda dan’uwa Ibrahim Suleiman Gwaram ya rubuta zai yi matukar amfani ga `yan’uwa musulmi. Na sami lokacin duba wannan littafi tun daga farkonsa har karshensa, kuma na gamsu da cewa marubucin yayi kokari ainun wajen kawo mas’alolin gado gwargwadon yadda za’a fahimta. Wannan littafi zai taimakawa `yan’uwa musamman wajen warware rikice-rikicen da akan ci karo da su in an zo rabon gado, saboda an rubuta shi cikin harshen Hausa kuma akwai karancin irin wadannan rubuce-rubuce a cikin harshen Hausa.

A wasu lokutan a kan sami ‘yan kura-kurai a wajen raba gado saboda karancin iliminsa, to amma wannan littafi zai taimaka wajen kawar da kura-kuran da ka taso.

Hakika rabon gado a cike yake da rikici, saboda haka Allah (SWT) shi da kansa ya bada ka’idojin da za’a bi a raba gado a cikin littafinsa mai tsarki (Alkur’ani) don haka bai barwa dan-Adam ya raba ba.

Allah (SWT) ya nufa, ba za’a raba gado cikin dadin rai ba, ko yaya sai rai ya baci. Wannan ta sanya wasu suke kin raba gado wai don kada hadin kan gida ya wargaje. To amma tun da Allah ya wajabta a raba to babu makawa sai an raba in ana so hadin kan gidan ya dore. In ko ba’a raba ba to zumuncin wannan gida ya gama mutuwa. Shi gado ana so a yi gaggawar

rabashi in da hali kafin ma a binne mamacin. Saboda tsananin kishi da Allah ya ke yi akan dukiyar marayu, tun daga nan duniya Allah yake kama maciya dukiyar marayu. A halin da muke ciki saboda son zuciya matsalar rabon gado tana daya daga cikin kararrakin da suka fi yawa a kotunmu. Magada ya kamata a rinka yin hakuri in an zo rabo. Domin a tuna an rasa wanda ya tara dukiyar ma bare abinda ya tara ya bari.

Daga karshe ina rokon Allah (SWT) ya sakawa dan'uwa Ibrahim Suleiman Gwaram da alhairi, kuma ya bashi kwarin gwiwa da juriya wajen irin wadannan rubuce-rubuce. Haka kuma ina rokon duk wanda ya karanta wannan littafi ya sanya marubucin cikin addu'oinsa na alheri.

Ustaz Haruna Hashim Gumel

Cheif Registrar, Shari'ah Court of Appeal

Dutse, Jigawa State

GABATARWA

Na fara da sunan Allah, mai rahama, mai jin kai. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halitta, mai rayawa, mai kashewa, Ubangijin da ya sanya mutuwa ta zama abar dandanawa ga kowane mai rai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugaban halitta Annabi Muhammad da alayensa da sahabbansa.

Bayan haka, ilmin rabon gado na daga cikin bangarorin ilmin da zai yi karanci a karshen zamani. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, a cikin ruwayar Imam Ahmad da Baihaki ya ce:

> *"ku nemi ilmin rabon gado, kuma ku sanar da shi ga mutane, domin za a dauke wannan ilmin kuma fitina ta bayyana a lokacin da mutum biyu za su saba a kan rabon gado, babu wanda zai iya raba tsakaninsu"*

Hakika, kwadaitarwar wannan Hadisin da kuma ganin yadda rikicin rabon gado ke karuwa a wannan zamani sun yi mini kaimi na ga ya dace im bada gudunmawata a wannan fanni a cikin harshen mu na Hausa.

Bayan wallafa littafi na farko, ga shi Allah Subhanahu wa-ta'ala ya bani ikon rubuta littafi na biyu. Rabon Gado Takaitacciyar Hanya littafi na biyu (2) ya kunshi babi-babi guda bakwai (7) wadanda suka shafi mas'alolin da Alkalai da kotunanmu su ke kishirwar yin nazari a kansu. Mas'aloli kamar rabon gado tare da wanda ya `bace ko gadon dan ciki ko gadon Zul-arham da sauransu an bayyana su a littafin gwargwadon fahimta. Ina fata Allah ya sa littafin ya zama mai amfani ga 'ya'uwa musulmi.

A karshe, ina rokon Allah ya yi min jagora akan tsara wannan littafi, tare da kakkabe duk wani kuskure da ka iya samuwa saboda ajizancin dan-Adam, amin. Wassalam

Ibrahim Sulaiman Gwaram
Ma'aikatar Ilmi,
Sashen Makarantun Kimiyya,
Jihar Jigawa
07030512212

BABI NA DAYA (1)

HUKUNCIN RABON GADON DA YA SHAFI MUNASAKHA

A littafi na farko, an kawo misalai da yawa akan yadda ake gudar da rabon gado a tebura. Saboda haka a nan ba zamu zurfafa bayanai akan yadda ake gudanar da rabo ba, sai dai zamu tafi kai tsaye, akan yadda ake warware mas'alar munasakha.

MUNASAKHA rabon gado ne wanda akan sami jinkirin gudanar da shi har sai da wani ko wasu daga cikin magada suka mutu.

Idan aka jinkirta rabon gado ba a gudanar da shi ba har sai da wani magaji ya mutu, to akan buga rabo a cikin tebur sai a cire kashin wannan mamaci a rabawa nasa magadan. Ka ga ashe za'a iya yin tebura guda biyu; daya na mamacin farko, daya teburin kuma na mamaci na biyun.

A karshe sai a dunkule rabon wadannan teburan a karkashin wata mas'ala sabuwa wacce zata tattare rabon dukkan magadan a wuri daya. Wannan sabuwar mas'ala ana cewa da ita , ***Jami'atut tas-hihi,*** ko a takaice **Jami'a.**

HALAYE UKU (3) NA RABON MUNASAKHA

1. **<u>A inda magadan mamacin na biyu su ne dai magadan mamacin farko</u>**

   A irin wannan hali akan shafe mamaci na biyun a rabawa shauran magadan dukiyar gaba daya.

MISALI

Mutum ne ya mutu ya bar 'Ya'ya maza su uku, kafin a raba gado sai daya daga cikin 'Ya'yan ya mutu. Wannan Da da ya mutu ba shi da wasu magada sai dai su wadannan 'Yan'uwa nasa biyu da suka rage.

Hukuncin anan shine za a kaddara shi Dan da ya mutu kamar babu shi, sai a rabe dukiyar ga 'Yan'uwansa su biyu. Duba tebur na 1 (1)

Tebur na 1 (1)

Magada		Mas'ala (2)
Da	YMT	0
Da		1
Da		1
		(2)

MANUFAR WADANNAN HARRUFA

YMT = Ya mutu

TMT = Ta mutu

MJB = Mah-jub, wato an kare magajin daga cin gado a wannan hali

MRM = Mah-rum, ko Mah-rumah idan magajin ba ya cikin masu cin gado a wannan hali.

2. **A inda magadan mamaci na biyu sune magadan mamaci na farko amma dangantaka ta canja**

A wannan hali za'a buga rabon mamacin farko a tebur, sai a dauki kashin mamaci na biyu a rabewa magadansa a wani teburin sabo.

Bayan haka sai a dunkule rabon teburan biyu a karkashin **Jami'a.**

Nan gaba kadan zamu koyi yadda ake dunkule rabon a karkashin Jami'a, inshaAllah.

MISALI:

Mutum ne ya mutu ya bar Matan aure biyu, Uwar gida ta na da Da daya namiji, amma Amarya ta na da ‘Ya’ya mata su uku (3), sai daya daga cikin ‘Ya’ya matan nan ta mutu kafin a raba gado.

Tantance magadan mamacin farko (mai gida) da magadan mamaciya ta biyu (wato wannan ‘Yar Amarya)?

AMSA

Magadan mai gida	**Magadan ‘Yar Amarya**
Matar Aure (Uwar Gida)	MRM
Matar Aure (Amarya)	Uwa
Da (Dan Uwar Gida)	Li’abbi
‘Ya’ya Mata biyu (na Amarya)	Shakikiya (2)
‘Yar Amarya (wacce ta mutu)	TMT

3. **<u>A inda magadan mamaci na biyu ba sune magadan mamacin farko ba</u>**

   A wani halin ma za ka iya samun magaji daya ya ci gado a bangaren mamacin farko sannan ya ci a bangaren mamaci na biyu.

   A irin wadannan halaye su ma akan gudanar da rabo a tebura biyu sannan a dunkule su a karkashin mas’alar Jami’a

   Za mu ga misalai a nan gaba kadan inshaAllah.

YADDA AKE GUDANAR DA RABON DA YA SHAFI MUNASAKHA

1. Da farko za ka gudanar da rabon gadon mamacin farko a cikin tebur, ka baiwa kowanne magaji kashinsa, daga cikinsu har da shi mamaci na biyu
2. Sai ka gudanar da rabon gadon mamacin na biyu ga magadansa a wani teburin sabo ka inganta mas’alar
3. Sai ka auna tsakanin kashin da mamacin na biyu ya samu (a tebur na farko) da mas’alar rabon gadonsa (a tebur na biyu)

4. Bayan ka auna za ka samu ko dai sun yi Tamasuli ko Tawafuki ko Tabayuni.
5. Za mu dauke su daya bayan daya mu ga yadda zamu samo Jami'a, sannan mu sauke kashin kowane magaji a karkashin Jami'ar, inshaAllah

(A) <u>Idan sun yi Tamasuli:</u>

Idan kashin mamaci na biyu (a teburin farko) yayi dai-dai da mas'alar rabon gadonsa (a tebur na biyu) abin ya zo da sauki

KAIDOJI

i. Sai ka dauki mas'alar rabon gadon mamacin farko (a tebur na farko) a matsayin Jami'a.
ii. Za ka tattare kashin da kowanne magaji ya samu a teburan biyu ka rubuta a karkashin Jami'ar.

MISALI

Mutum ne ya mutu ya bar:

i. 'Ya'ya mata uku (3)
ii. Shakikiya biyu (2)
iii. Shakiki

Kafin a yi rabon gadon sai daya daga cikin Shakikai matan nan ta mutu ta bar su wadannan 'Yan'uwa nata ; wato, Shakiki da Shakikiya. Nuna rabon a tebur.

AMSA

1. <u>Gudanar da rabon a cikin tebura biyu</u>
   Idan ka gudanar da rabon mamacin farko za ka ga mas'alar ta inganta akan talatin da shida (36), haka idan ka gudanar da rabon mamaciya ta biyu (wato shakikiya) mas'alar rabon ta kama uku (3) duba tebur na 1 (2) da ke kasa
2. <u>Nemo Jami'a</u> wato mas'alar da ta dunkule rabon teburan biyu a wuri daya.

a) <u>Auna</u> tsakanin kashin shakikiyar da ta mutu a tebur na farko (3) da mas'alar rabon gadon ta a tebur na biyu (wato uku (3)).

Idan ka auna za ka ga sun yi dai-dai tamasuli.

b) Saboda haka sai ka dauki mas'alar rabon mamacin farko (36) a matsayin Jami'a

3. <u>Sauke kashin kowane magaji a karshin Jami'a.</u> Duba tebur na 1 (2)

Tebur na 1 (2)

(12) **Jami'a**

			(3)	(36)				(3)	(36)
(3)	"Yaya Mata (3)	2/3	2	24		MRM		0	24
	Shakikiya			3		TMT		0	0
(4)	Shakikiya	AS	1	3		Shakikiya	AS	1	3+1
	Shakiki			6		Shakiki		2	6+2
			(3)	(36)				(3)	(36)

Kowacce 'Ya mace ta na da kashi 8, 24/3 = 8

Tambaya ta 1 (1)

Mutum ne ya mutu ya bar:-

(i) Matar aure
(ii) Uba
(iii) Uwa
(iv) "Yar-da

Kafin a raba gado sai wannan 'Yar-da ta mutu ta bar:-

(i) Mijinta
(ii) Uwa
(iii) 'Yaya mata uku (3)
(iv) 'Yaya mata biyu (2)

Raba gadon wadannan mamata ka dunkule rabon a karkashin Jami'a.

B. Idan sun yi Tawafuki

Lambobi biyu sun yi Tawafuki idan an sami wata karamar lamba wacce za ta iya shiga kowannensu ba tare da ragowa ba. (Common factor).

Idan kashin magaji na biyu (a teburin farko) ya yi Tawafuki da mas'alar rabon gadonsa (a tebur na biyu) ga yadda za ka yi:-

KA'IDOJI

1) Nemo karamar lambar da za ta iya shiga kashin mamaci na biyu da kuma masalar rabon gadon nasa (wato common factor).
2) Nemo Wafkin kashin mamaci na biyu

$$= \frac{kashin\ mamacin}{common\ \ factor}$$

Sai ka buga wannan wafkin akan mas'alar rabon gadonsa (a tebur na biyu)

3) Nemo wafkin mas'alar rabon gadon mamaci na biyu

$$= \frac{mas'alar\ rabon\ gakdon}{common\ \ factor}$$

Sai ka buga wannan wafkin akan mas'alar rabon gadon mamaci na farko (a tebur na farko):- wannan ita ce Jami'a

4. Sauke kashin kowane magaji a karkashin Jami'a.

Misali

Mace ce ta mutu ta bar:

(i) Miji
(ii) ‘Ya
(iii) Dan-da
(iv) ‘Yar-da

Kafin a raba gado sai Mijin ya mutu ya bar:-

(i) Matar aure
(ii) Uwa
(iii) ‘Yan uwa mata (2) Liabbai
(iv) Dan’uwa Li-ummi

TEBUR NA 1 (3)

(3) (5) (1)

Jami’a

		(4)	(12)			~~(12)~~ (15)	(60)
Miji	1/4	1	3	YMT		0	0
‘Ya	1/2	2	6				30
Dan-da	AS	1	2				10
‘Yar-da			1				5
		(4)	(12)	Matar Aure	1/4	3	3
				Uwa	1/6	2	2
				Li’abbiy (2)	2/3	8	8
				Li’ummi	1/6	2	2
						(15)	(60)

Jami’a = 5x12
= 60

(i) Kashin mamaci na biyu, wato miji, a teburin farko = 3

(ii) Mas”alar rabon gadonsa a tebur na biyu = 15.

(iii) Idan ka auna za ka ga kashinsa, wato uku (3) sun yi tawafuki da mas’alar rabon gadonsa, wato goma sha biyar (15) a cikin karamar lamba 3.

(iv) Wafkin kashin $= 3/3 = 1$

Buga wannan wafkin (1) akan mas'alar abon gadonsa (a tebur na biyu). Duba tebu na 1 (3).

(v) Wafkin Mas'alar rabon gadon = 15/3 = 5.

Buga wannan wakafin (5) akan mas'alar rabon gadon mamacin farko (a tebur na farko).

Jami'a = 5x12 = 60.

Sittin (60) ya zama mas'alar Jami'a, duba tebur .

(vi) Sauke kashin kowanne magaji a karkashin Jami'a.

Tambaya ta 1 (2)

Mutum ne ya mutu ya bar:-

i. Uwa = $\frac{1}{6}$

ii. Uba = $\frac{1}{6}$, As

iii. Matar aure = $\frac{1}{8}$

iv. "Yaya mata (5) = $\frac{2}{3}$

Sai aka sami jinkirin rabon gado har Uban ya mutu ya bar:-

i. Matar aure = $\frac{1}{4}$

ii. "Yar uwa shakikiya = $\frac{1}{2}$

iii. Dan uwa li'ummi = $\frac{1}{6}$

iv. Dan-dan'uwa shakiki = AS

Nuna rabon gadon tare da ajiye kashin kowane magaji a karkashin Jami'a.

C. Idan sun yi Tabayuni

Idan ya kasance a tsakanin kashin mamaci na biyu (a teburin farko) da mas'alar rabon gadonsa (a tebur na biyu) sun yi Tabayuni, to, ga yadda za ka yi:

KA'IDOJI

1. Kai tsaye sai ka buga mas'alar rabon gadon mamaci na biyu akan mas'alar rabon gadon mamaci na farkon (wato akan teburin farko). Duk abinda ya ba ka shine mas'alar Jami'a.
2. Sannan ka buga kashin da mamaci na biyu ya samu akan mas'alar rabon gadonsa (a teburin na biyu)

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da 'Ya'yanta guda uku; daya namiji, biyu mata. Bayan haka ya bar wata 'Ya wacce uwarta ba ta tare da shi a lokacin da ya mutu.

Kafin a raba gado sai wannan matar tasa ta mutu ta bar wadannan 'Ya'yan nata su uku (3). Tace magadan ka raba gadon , ka baiwa kowanne magaji kashinsa a karkashin Jami'a.

AMSA

(1) Tace magadan ka gudanar da rabon a tebura biyu.

(2) Auna tsakanin kashin matar auren wato (5) da mas'alar rabon gadonta, wato (4), za ka ga sun yi Tabayani.

(3) Saboda hakan sai ka buga (4) akan mas'alar rabon mamacin farko, wato akan (40) . Duba tebur

Jami'a = 4x40 = 160

(4) Sannan ka buga (5) akan masa'alar Matar auren a tebur na biyu, wato akan, (4). Duba tebur na 1(4)

Tebur na 1 (4)

(5) (4) (5) Jami'a

		(8)	(40)	/			(4)	160
Matar Aure *	1/8	1	5	/	TMT		0	
Da *			14	/	Da *		2	56+10
'Ya *	AS	7	7	/	'Ya *	AS	1	28+5
'Ya *			7	/	'Ya *		1	28+5
'Ya			7	/	MRM		0	28
		(8)	(40)	/			(4)	(160)

(5)

Auna (4) da (5) – Sun yi Tabayuni

Jami'a = 4x40 = 160

<u>TAMBAYA TA 1 (3)</u>

Mace ce ta mutu ta bar:-

i. Miji
ii. 'Yaya mata biyu (2)
iii. Uwa
iv. Uba

Sai mijin ya mutu kafin ayi rabon gadon ya bar:

i. "Yar'uwa Shakikiya
ii. Uwa
iii. Matar Aure
iv. Dan'uwa Li'ummi

Raba gadon, ka nuna kashin kowanne magaji a karkashin Jami'a .

(D) **Misali akan rabon munasakha a inda mutane da yawa su ka mutu kafin a raba gado**.

Misali Mutum ne ya mutu ya bar dukiyarsa kimanin (N 3,600,000) kuma ya bar magada kamar haka:

i. Matan aure (3)
ii. 'Ya'ya mata (3)
iii. Shakikai mata (2)
iv. Li'ummai mata (2)

Kafin a raba dukiyar sai daya daga cikin Matan nasa ta mutu ta bar:

i. Uwa,
ii. Uba,
iii. 'Ya,
iv. 'Yar-da,
v. Li'ummi

Sannan kuma Uwar ta mutu ta bar

(i) Kaka Uban-uba, (ii) 'Ya'ya mata (3)

AMSA

1. A wannan rabo an kare Li'ummai saboda samuwar reshe, wato, 'Ya (ko 'Yar-da).
2. Gudanar da rabon mamacin farko da kuma na mamaciya ta biyu (wato, gadon Matar aure).
3. **Nemo Jami'ar farko**

Auna kashin Matar aure (6) da mas'alar rabon gadonta (6) – sun yi Tamasuli. Saboda haka mas'alar Jami'a ta kama 144. Duba tebur. Sauke kashin magadan a karkashin Jami'a ta farko.

4. Raba gadon mamaciya ta uku (wato, Uwa) ka inganta mas'alar.
5. **Nemo Jami'a ta biyu**

   Auna kashin rabon Uwa, wato, (1) da mas'alar rabon gadonta a tebur na uku (3), wato, goma sha takwas (18)

   Auna (1) da (18) za ka ga sun yi tawafuki a cikin lamba (1).

   Buga (18) a bisa Jami'ar farko (144)

   Jami'a ta biyu ta kama = 18x144 = 2,592

6. Sauke kashin duk magadan a karkashin Jami'a ta biyu.
7. **Nemo Juzu'it-tarikah**

   Juzi'i = ₦ 3,600, 000/2,592

   = ₦ 1, 389

8. Buga wannan Juz'i akan kashin magadan ka baiwa kowa hakkinsa na dukiya. Duba tebur na 1 (5)

TEBUR NA 1 (5)

TEBUR NA 1 (5)

			Jami'ar Farko								Jami'a ta biyu			
			(6)					(18)			(3)	(1)		₦1, 389
			(24)	(144)			(6)	(144)			(6)	(18)	(2,592)	(₦3,600,000)
	Matar aure (3)	1/8	3	18	TMT=6			12					216	₦300,024
(3)	'Ya'ya mata (3)	2/3	16	96				96					1,728	₦2,400,192
(2)	Shakikiya (2)	As	5	30				30					540	₦750,060
			(24)	(144)	Uwa	1/6	1	1	TMT				0	0
					Uba	1/6 (AS)	1	1					18	₦25,002
					'Ya	½	3	3					54	₦75,006
					'Yar-da	1/6	1	1					18	₦25,002
							(6)	(144)	Uban-uba	1/6 AS	2	6	6	₦8,334
								(3)	'Yaya mata (3)	2/3	4	12	12	₦16,668
											(6)	(18)	(2,592)	₦3,600,000

Activa

BABI NA BIYU (2)

FITA DAGA CIN GADO (ATTAKHARUJ)

At-takharuj mas'laha ce tsakanin magada yadda wani daga cikin magada zai yarda ya sarayar da hakkinsa na gado. Manufa, ita ce, shi wannan magaji ya fitar da kansa daga cin dukiyar wannan gado, wato ya yafe dukkan hakkinsa ko wani sashe na hakkinsa na gadon.

Wannan hukunci ya tabbata ga shari'a domin an rawaito cewa Matar Abdurrahman dan Auf (R.A) mai suna Tumadhir 'yar As-bagu ta sarayar da hakkinta na durhami dari ga kishiyoyinta su uku. Wato, ta fita daga cin gado, ta bar wannan adadin kudi aka rabe shi ga kishiyoyinta su uku.

Idan aka sami wani magaji ya fita daga cin gado za'a raba kashinsa ga wadanda ya baiwa a cikin shauran magadan.

Magaji zai iya fita daga cin gado ya bar kashinsa a raba shi ko dai ga:

- Dukkan abokan rabo, ko kuma ga
- Wasu daga cikin abokan rabo, ko kuma ga
- Wani abokin rabo shi kadai

A) Yadda ake raba kashin da aka yi sulhu a kansa ga dukkan abokan rabo

KA'IDA

Za'a buga rabo a inganta mas'alar sannan a juyar da kashin wanda ya fita daga cin gadon a rabawa sauran abokan rabo. Za'a baiwa kowanne magaji irin abinda ya ci na farali (kamar dai an yi raddi). A kan dauki jumlar kashin sauran magada a matsayin sabuwar mas'alar rabo.

MISALI:

Mutum ne ya mutu ya bar Uba da ´Ya da Matar aure. Ya mutu ya bar gida da kudi naira miliyan arba'in da dubu dari biyu (N40,200,000). An yi sulhu a kan cewa matar auren za ta rike wannan gida sannan ta fita daga cin gadon wannan kudi. Nuna rabon a teburi?

TEBUR NA 2 (1)

N1,914,286 Tarikah

Magada	Rabo	(24)	(21)	N 40,200,000
Matar aure	1/8	3	0	0
“Ya	1/2	12	12	N 22,971,429
Uba	1/6 (As)	9	9	N 17,228,571
		(24)	(21)	N 40,200,000

- Uba ya ci gado farlan-wa-ta’asiban
- An fitar da kashin matar aure, wato kashi uku (3) an rabe shi ga Uba da ´Ya
- Jumlar kashin magada = 12 + 9 = 21
- Sabuwar mas’alar rabo= 21
- Juz´u tarikah =Tarikah/mas’alar rabo
  = N 40,200,000/21
  = N 1,914,286

B) Yadda ake raba kashin da aka yi sulhu a kansa ga wasu daga cikin abokan rabo

Ka’ida

Za a raba dukiyar a tebur, a inganta mas’alar, sannan a juyar da kashin wanda ya fita daga cin gado ga magajin da aka yi sulhu da shi. Wato wannan magaji zai ci gado kashi biyu; daya na sa na asali, daya na sulhu.

MISALI:

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da “Ya“ya maza biyu (2) da kuma “Ya mace. Sai daya daga cikin “Ya“ya mazan ya yi sulhu da wannan “Ya mace a kan ta bar masa na ta kashin, kuma ta yarda. Nuna wannan rabo a cikin tebur?

TEBUR NA 2 (2)

		(5)		
Magada	Rabo	(8)	(40)	(40)
Matar Aure	1/8	1	5	5
‘Da	As	7	14	14
‘Da			14	14+7
‘Ya			7	0
		(8)	(40)	(40)

BABI NA UKU (3)

RABON GADO GA ZUL-ARHAM

Zul-arham dangi ne da suke da zumunta da mamaci amma ba sa cin gado da farali kuma ba sa cin gado da asibci.

Misali

i. Goggo (kanwa ko yar-Uba)
ii. Kawu (kani ko wan-Uwa)
iii. Umma (kanwa ko yar-Uwa)
iv. Dan 'ya
v. Dan 'yar-uwa

Sahihancin bayarda dukiyar gado ga zul-arham ya fuskanci ij-tihadi a tsakanin Sahabbai da kuma Tabi'ai. Akan haka malaman maz'haba su ka rabu bangarori biyu.

Bangaren farko suna ganin cewa idan babu masu cin gado da farali, kuma babu asibai to za'a mika dukiyar gado ga baitul- mali don amfanin musulmi gaba daya. Wannan ita ce maz'habar Imam malik da Imam Shafi'i, Allah ya yi musu rahama. Amma maz'habobin Abu-Hanifa da Ahmad dan Hambali sun dogara akan cewa a rashin magada masu cin farali ko asibci za a iya raba dukiyar gado ga zul'arham. Kowanne bangare daga bangarorin nan biyu ya kawo hujjojinsa.

Hujjojin masu ra'ayin kada a baiwa Zul'arham gado

1) Sun kafa hujja da cewa nassin alkur'ani ko Hadisai ba su ambaci gadon Zul'arham ba saboda haka babu wani dalili da zai sa a basu gado.
2) Haka kuma an taba tambayar Manzon Allah (S.A.W) akan ko za a iya baiwa Goggo da Umman mamaci gado ? Sai ya ce,"Jibrilu ya sanar da ni cewa ba su da gadon komai…" Wannan ya nuna ashe tun da Goggo da Umma ba su da gado, za a yi kiyasin cewa duk sauran Zul'arham ma ba su da gado.
3) Idan aka baiwa Baitil- mali dukiyar gado,to, duk al'ummar musulmi za su amfana,amma idan Zul'arham aka baiwa, amfanin dukiyar ya tsaya ga mutane 'yan kalilan. A ka'idar Fiq'hu kuwa, akan gabatar da mas'lahar al'umma akan mas'lahar 'yan-tsirari. Don haka Baitil-malin musulmi shi ya fi cancanton ya ci gado , ba Zul'arham ba.

Hujjojin masu ra'ayin a baiwa Zul'arham gado

1) Sun kafa hujja da cewa, ayoyin alkur'ani da su ka yi umarnin a raba gado sun nuna cewa ,"Dangi su suka fi cancanton su ci gado a tsakaninsu." Ayoyin sun ambaci dangi mud-lakan babu wata ka'ida, saboda haka ashe dangi anan sun hada har da Zul'arham.Matukar babu masu cin gado da farali ko asibci, to, Zul'arham za su ci gado.
2) A zamanin Manzon Allah (S.A.W) wani Sahabi mai suna Thabitu dan Dahadaha ya mutu bai bar magada ba sai Dan 'yar'uwarsa, mai suna Abu Lubanata,Manzon Allah ya ce, Ku baiwa Abu Lubana gadon dukiyar. Dan 'yar'uwa ya na cikin Zul'arham.
   Bayan haka an ruwaito Khalifa Umar dan khadab yana cewa Manzon Allah (S.A.W) ya ce, "Khala, magaji ne ga mamacin da ba shi da magada." Khala shine Kawu, Kani ko wan Uwa. Wadannan hujjoji sun tabbatar da gado ga Zul'arham.
3) Dangantakar baitil-mali da mammaci dangantaka ce ta musulunci kawai, amma zul-arham su na da dangantaka ta musulunci da kuma ta zumunta da mamacin. Saboda haka zul-arham sun fi kusaci da mamacin akan baitil-mali, kuma su suka fi cancanton su ci gado.

Idan ka auna hujjojin kowane bangare za ka samu cewa masu ra'ayin a baiwa zul-arham gado sun kawo dalilai masu karfi. Sannan kuma masu ra'ayin a mika dukiyar gado ga baitil-mali sun bada sharadin cewa lallai baitil-malin ya zama mai tsari kuma ya zamanto ana sarrafa dukiyar ta hanyar da ta dace, akan adalci. Ganin cewar a wannan zamani babu wasu baitil-mali masu tsari a kasashen musulmi, jam-hurun malamai su ka yi fatawa akan bayar da gado ga zul-arham. Wannan fatawa ta sami karbuwa tun kimanin karni na uku bayan Hijra izuwa zamanin da muke ciki a yau. Akan haka, a wannan littafi namu zai duba yadda ake rabawa zul-arham dukiyar gado.

Sharrudan cin gadon zul-arham

Kafin ma'abucin zumunta ya ci gado lallai wadannan sharudda su cika:

1) Ya kasance babu wani magaji mai cin gado da farali. Domin idan akwai mai cin gado da farali za'a fara bashi kashinsa na farali, sannan idan akwai shauran dukiya (mabakiya) sai ayi raddinta a gareshi. Ka tuna ma'aurata (miji ko mata) ba a yi musu raddi.
2) Ya kasance babu wani mai cin gado da asibci.
   Idan akwai asibi zai ci dukkan dukiya idan ya kadaita ko kuma ya kwashe shauran dukiya da ta rage (mabakiya)

3) Idan miji ko matar aure su ka ci gado,sai aka sami mabakiya kuma babu wasu magada masu cin raddi sai Zul'arham ,to, za'a bayarda wannan mabakiya ga zul-arham . Ana fifita zul-arham akan yin raddin mabakiya ga miji ko matar aure.

Yadda ake rabawa zul-arham dukiyar gado

Akwai hanyoyi uku (3):

1) Maz-habar Ah-lur-rahimi

Malaman wannan hanya ta rabawa zul-arham gado sun yi la'akkari da zumunta kawai. Su kan ce ai kowanne daga cikin magadan zumunci ne ya hadasu. Saboda haka za'a raba musu dukiyar gado dai-dai wa daida. Babu banbanci tsakanin namiji da mace kuma ba a duba kusancin magajin da mamacin.

2) Maz-habar Ah-lul 'karaba

A wannan maz-habar akan dauki zul'arham a matsayin Asibai.Akan duba karfin dangantakarsu da mamacin da kuma darajarsu, sai a raba su jinsi-jinsi.

A kawane jinsi za a raba gadon dukiyar a bada rabon namiji daya dai dai da rabon mata biyu (kamar dai asibai).

3) Maz-habar Ah-lut-Tanzil

A wannan maz-haba da ta shahara akan leka can baya a duba asalin magaji mai ci da farali ko asibci wanda ya jona shi Zul'arham din da mamacin. Sai a kaddara Zul'arham din a matsayin wannan magaji mai ci da farali ko asibcin. Saboda haka sai a bashi irin rabon da wannan magaji mai ci da faralin ko ci da asibcin zai ci na gado.

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Goggo (kanwa ko yar-Uba) a matsayin magajiya. To sai a dauki ita wannan Goggo a matsayin Uba ga mamacin. Saboda haka sai a bata rabo irin na Uba. Wato sai ta ci gadon da asibci ko sudusin dukiya.

Rabo ta irin wannan hanya ya kwatanta abin da ya zo a cikin nassin alku'ani da Sunna, don haka maz-habar ta fi karbuwa a wajen malamai.

A tebur na kasa zamu kawo matsayin da za a kaddara dangantar Zul'arham da mamacin da kuma irin rabon da za a bashi.

Tebur: 3(1) Mai nuna Matsayin da za a dauki zul-arham ga mamacin da kuma Rabon da za a bashi na gado.

LMB	Zul-arham din da zai ci gado	Matsayin da za a dauke shi ga mamacin	Rabon da za a ba shi
1	Dan 'Ya (wa-in-safala)	'Ya	$^1/_2$
2	'Yar 'Ya (wa-in-safalat)	'Ya	$^1/_2$
3	'Ya'yan 'Ya (maza ko mata)	'Ya'ya mata (na tsatso)	$^2/_3$
4	Dan 'Yar-da	'Yar-da	1/2, 1/6
5	'Yar 'yar-da	'Yar-da	1/2, 1/6
6	'Ya'yan 'Yar-da (maza ne ko mata)	Jikoki 'Ya'yan-Da (mata)	$^2/_3$
7	Goggo (Kanwa ko yar- Uba, mud-lakan)	Uba	AS , 1/6
8	Kawu (Kani ko wan- Uwa, mud-lakan)	Uwa	1/3, 1/6
9	Umma (Kanwa ko yar- Uwa, mud-lakan)	Uwa	1/3, 1/6
10	Uban Uwa (wa-in-ala)	Uwa	1/3, 1/6
11	Uwar Uban-Uwa (wa-in-alat)	Uwa	1/3, 1/6
12	Dan 'Yar-uwa (shky ko li'abby)	Shky	1/2, AS
		Li'abby	1/2, 1/6, AS
13	'Yar 'Yar-uwa (Shky ko li'abby)	Shky	1/2, AS
		Li'abby	1/2, 1/6, AS
14	'Ya'yan 'Yar-uwa (Mud-lakan)	'Yan-uwa (mata)	2/3
15	'Yar dan-uwa (Shakiki ko li'abbi)	Shakiki ko li'abbi	AS
16	Dan dan-uwa (Li'ummi ko li'ummiya)	Li'ummi ko li'ummiya	1/6
17	'Yar dan-uwa (Li'ummi ko li'ummiya)	Li'ummi ko li'ummiya	1/6
18	'Ya'yan 'Yan-uwa	Li'ummai	1/3

19	‘Yar baffa (shakiki ko Li’abbi)	Baffa (shakiki ko Li’abbi)	AS

Misalai

1) Mutum ne ya mutu ya bar goggo da cikin ummarsa sune kadai magada. Nuna rabon da za a baiwa kowacce magajiya.

Amsa

A mah-mabar Ah-lul Tanzil za’a dauki goggo a matsayin Uba ga mamaci, ita kuwa Umma a matsayin Uwa.

Tebur: 3(2)

Zul-arham (Magaji)	**A matsayin**	**Rabo**	**Mas’ala (3)**
Goggo	Uba	AS	2
Umma	Uwa	$^1/_3$	1

Za a baiwa Uba $^2/_3$ sannan Uwa $^1/_3$ na dukiya.

2) Mutum ne ya mutu ya bar ‘Yar-‘ya da Dan ‘yar-uwa shakikiya da ‘Yar dan’uwa li’abbi. Nuna irin rabon da za’a baiwa kowane magaji.

Amsa

Ta hanyar Ah-lul-Tanzil, zamu nuna rabon a tebur na 3(3).

Tebur na 3(3)

Zul-arham (Magaji)	**Matsayinsa ga mamacin**	**Rabo**	**Mas’ala (2)**
‘Yar ‘ya	‘ya	$^1/_2$	1
Dan ‘Yar-uwa (shky)	Shakikiya	AS	1
‘Yar li’abbi	Li’abbi	MJB	0

Za’a baiwa ‘yar’ya $^1/_2$, Dan shakikiya $^1/_2$ (asiba tare da ‘ya). Dan shakikiya ya ture ‘yar li’abbi daga cin gado.

3) Mutum ne ya mutu ya bar Zul-arham sune kadai masu cin gado. Magadan sun hada da
   i. ‘Yar-‘ya = ‘Ya
   ii. Dan ‘yar-uwa shakikiya = Shakikiya

iii. Dan ‘yar-uwa li’ummiya = Li’ummiya
iv. ‘Yar dan-uwa li’abbi = Li’abbi

Amsa

- Shakikiya ta zama asiba tare da ‘Ya kuma ta ture li’abbi
- ‘Ya ta ture li’ummiya daga cin gado
- Saboda haka masu cin gado sun rage ‘ya da shakikiya

Tebur na 3(4)

Zul-arham (Magaji)	A matsayin	Rabo	Mas’ala (2)
‘Yar-‘ya	‘Ya	$^1/_2$	1
Dan ‘yar-uwa shakikiya	Shakikiya	$^1/_2$	1
Dan ‘yar-uwa li’ummiya	Li’ummiya	MJB	0
‘Yar dan-uwa li’abbi	Li’abbi	MJB	0

4) Mace ce ta mutu ta bar wadannan zul-arham a matsayin magada:
   i. ‘Yar ‘yar-uwa shakikiya
   ii. ‘Yar yar’-uwa li’abbiya
   iii. Dan ‘yar-uwa li’ummiya
   iv. ‘Yar baffa shakiki

Nuna rabon a cikin tebur

Amsa

Tebur na 3(5)

Zul-arham (Magaji)	A matsayin	Rabo	Mas’ala (6)
‘Yar shakikiya	Shakikiya	$^1/_2$	3
‘Yar li’abbiya	Li’abbiya	$^1/_6$	1
Dan li’ummiya	Li’ummiya	$^1/_6$	1
‘Yar baffa	Baffa	AS	1

BABI NA HUDU (4)

RABON GADO TARE DA MAGAJI MATA- MAZA
(AL- KHUNSA)

Mata-maza wasu jinsin mutane ne da akan haifa dauke da al‘aurar maza da ta mata gaba daya. Sun banbanta dangane da irin rikicewar lamarinsu. Wani mata-mazan ma zai iya kasancewa ba shi da al‘aurar gaba dayansu.

Mata-maza ya kan ci gado, haka kuma ana cin gadon dukiyarsa. To amma rabon gado tare da magaji mata-maza ya kan bukaci a tantance ko dai mata-mazan yafi karfi a bangaren maza ko kuma yafi karkata ya zuwa bangaren mata. Idan har an tantance shi, to, lamari ya saukaka, sai a bashi irin rabon da ya cancanci a bashi; rabon namiji ko rabon mace. Amma idan mata-maza ya tabbata mush-kili, ma’ana, an kasa fahimtar ko shi namiji ne ko mace ce, to akan gudanar da rabo a bisa karantarwar ma’abuta ilimi kamar yadda abin zai zo a nan gaba kadan in Allah ya so.

TANTANCE MATA –MAZA A MATSAYIN NAMIJI KO MACE

Akan yi irin wannan tantancewa ta hanyar lura da abubuwa guda biyu:

1. Lura da mafitar fitsari, sannan
2. Lura da yanayin balagarsa.

Ga matakannan daya bayan daya:

1. Farko za`a lura da al`aurar da ya ke yin fitsari da ita. Idan yana fitsari ta azzakarinsa to ya zama namiji, idan kuwa ya na fitsari ta farji to ya zama mace.
   Amma idan aka samu cewa ya kan yi fitsari ta dukkannin al‘aurorinsa biyu, to mataki na gaba shine;
2. Sai a lura da kafar da yafi yin amfani da ita wajen yin fitsarin. Misali, idan a cikin yini guda ya kan yi fitsari har sau hudu ta azzakari amma sau daya ta farji to ya zama namiji (duba akasin haka).
   Amma idan yawan yin fitsarinsa ta kafofin biyu suka yi dai-dai, to matakan gaba sune;
3. Sai a lura da kafar da fitsarin ya ke riga fitowa. Misali, idan ya na fara fitowa ta farji ya zama mace (duba akasin haka).
   Amma idan aka fahimci fitsarin ya na fitowa ta kafofin biyu a lokaci guda, to ;

4. Sai dai a shaurari balagarsa. Anan a kan tantance shi a matsayin namiji idan ya fitar da maniyyi koda a mafarki ne ko kuma an ga gemu ya tsiro a habarsa. Mata-maza ya na kasancewa mace idan nono irin na mata ya tsiro a kirjinsa, ko kuma idan ya wanke jinin haila.
   Amma idan har aka kasa tantance shi bayan an bi duk wadannan matakai da ke sama to mata-maza ya tabbata mush-kili.

DANGANTAKAR MATA-MAZA MUSH-KILI DA MAMACI

A bisa shari'a ba ya halatta Mata-maza ya yi aure ko a aure shi matukar yana mush-kili har sai an tantance shi. Saboda haka Mata-maza mush-kili ba zai iya zama Miji ko Matar aure ga mamaci ba. Haka kuma, tunda ba ya haifuwa ba zai zama Uwa ko Uba ko Kaka ga mamaci ba. Amma an samu zai iya kasancewa daya daga cikin dangogin nan guda bakwai (7):- Da, Jika, Dan'uwa, Dan-dan'uwa, baffa, Dan-baffa, ko mawali.

YADDA AKE RABA GADO TARE DA MATA-MAZA BISA KARANTARWAR IMAM MALIK

Akan buga rabo a cikin tebura guda biyu; tebur na farko akan kaddarawar shi Mata-mazan namiji ne, tebur na biyu akan kaddarawar shi mace ce. Akan buga lissafi a inganta dukkan mas'alolin guda biyu.

A wannan maz'haba akan baiwa kowanne magaji rabin kashin da ya samu a kaddarawar khunsa namiji $\left(\frac{NMJ}{2}\right)$. Sannan a kara ba shi rabin kashin da ya samu a kaddarawar khunsa mace $\left(\frac{MC}{2}\right)$.

Fomula

Jumlar kashin kowanne magaji

$$= \left(\frac{NMJ}{2}\right) + \left(\frac{MC}{2}\right)$$

Yi nazarin wadannan ka'idoji guda biyar tare da Misalan da za'a kawo domin ka fahimci yadda ake rabon gado tare da Mata-maza.

Ka'idoji

1. **GUDANAR DA RABON A TEBURA BIYU;**
   Tebur na farko akan kaddarawar khunsa namiji ne, tebur na biyu akan kaddarawar khunsa mace ce.
   Inganta mas'alolin guda biyu.
2. **AUNA TSAKANIN MAS'ALOLIN RABON**
   Wato ka auna tsakanin mas'alar rabon khunsa namiji da mas'alar rabon khunsa mace. Idan ka auna sai ka lura cewa sun yi Tabayuni ne ko Tawafuki. Zamu kawo misalai.
3. **NEMO JAMI'A**
   Wato mas'alar da za ta hada rabon da aka yi na cikin teburan nan biyu, ta dunkule shi gu daya.
   a. **Tabayuni**
      Idan asalin mas'alolin nan guda biyu sun saba (Tabayun), za ka buga daya cikin daya sannan ka ninka wannan adadi. Duk abinda ka samu shine mas'alar Jami'a.
   b. **Tawafuk**
      Idan wadannan mas'alolin guda biyu sun yi Tawafuki a cikin wata karamar lamba, za ka nemo wafkin daya sannan ka buga shi cikin dayar. Za ka ninka wannan adadi don samun Jami'a. Za mu kawo misalai.
4. **NEMO JUZ'US SAHAMI**
   Wato lambar da za ka rubuta a bisa asalin mas'alar. Za ka buga wannan Juzu'i cikin abin da ke hannun kowanne magaji don samun kashinsa a wannan kaddarawa.

$$Juz'i = \left(\frac{Jami'a}{Asalin\ mas'ala}\right)$$

5. **NEMO KASHIN KOWANNE MAGAJI**
   Za ka nemo kashin magaji a bangarorin biyu, sannan ka ce:-

$$Jumlar\ Kashin\ Magaji = \left(\frac{NMJ}{2}\right) + \left(\frac{MC}{2}\right)$$

   Sannan sai ka rubuta jumlar kashin wannan magajin a karkashin Jami'a.

Misalai

Misali na daya (1)

Mutum ne ya mutu ya bar 'Ya'ya biyu maza , daya sahihi , dayan kuma khunsa. Nuna rabon gadon a tebur.

Amsa

Gudanar da rabon a tebura biyu; a kaddarawar khunsa namiji sannan a kaddarawar khunsa mace.

i. **Kaddarawar khunsa namiji**
   Asalin mas'alar, Da (sahihi) da kuma Da (khunsa) shine biyu (2), kowannensu za'a ba shi kashi daya a hannunsa.
ii. **Kaddarawar khunsa mace**
   Asalin mas'alar Da (sahihi) da 'Ya (khunsa) shine uku (3). Da (sahihi) yana da kashi biyu (2), 'Ya (khunsa) tana da kashi daya (1) .

Duba tebur na hudu 4 (1)

- <u>Auna tsakanin mas'alolin biyu</u>
  Mas'alar farko = 2
  Mas'ala ta biyu = 3

Biyu (2) da Uku (3) sun saba (tabayun)

- <u>Nemo mahadar mas'alolin biyu (Jami'a)</u>
  Buga mas'alar farko biyu(2) cikin mas'ala ta biyu uku(3) sannan ka ninka adadin
  Jami'a = 2x3x2

  = 12

Za ka rubuta goma sha biyu (12) a teburin mahadar rabo (wato, teburin Jami'a)

- <u>Nemo Juzu'us sahami</u>

Wato lambar da za ka buga cikin abinda ke hannun kowanne magaji don samun kashinsa a wannan kaddarawa.

<u>Mas'alar farko</u>

$$Juzu'i = \frac{jami'a}{asalin\ mas'alar} = \frac{12}{2} = 6$$

Rubuta shida akan asalin mas'alar farko (2). Zaka buga wannan shida (6) cikin abinda ke hannun kowane magaji don samun kashinsa a kaddarawar khunsa namiji.

Mas'ala ta biyu

$$Juzu'i = \frac{12}{3} = 4$$

Rubuta hudu a saman aaslin mas'alar (3). Buga hudu (4) cikin abinda ke hannun kowanne magaji don samun kashinsa a kaddarawar khunsa mace

- Nemo kashin kowanne magaji
  Duba tebur na 4 (1)
  A) **Kashin Da Sahihi**

A kaddarawar kunsa namiji = 6x1

Rabi ya kama 6/2 = 3

A kaddarawar khunsa mace = 4x2 =8

Rabi ya kama 8/2 = 4

Jimlar kashinsa = 3+4 = 7

Rubuta bakwai (7) a karkashin Jami'a a gidan Da sahihi. Duba tebur

B) Kashin Da khunsa

A kaddarawar khunsa namiji= 6x1=6
Rabi ya kama; 6/2=3
A kaddarawar khunsa mace =4x1=4
Rabi ya kama; 4/2=2
Jumlar kashinsa=3+2=5
Rubuta biyar (5) a karkashin Jami'a a gidan Da khunsa

Idan ka tara bakwai (7) da biyar (5) zai baka goma sha biyu (12). Rabo ya yi dai dai. Duba tebur,

Tebur na 4(1)

Kaddarawar Khunsa namiji		kaddarawar khunsa mace		
	6		4	Jami'a
	Asalin (2)		Asalin (3)	Ingancin (12)
Da (sahihi)	1	Da (sahihi)	2	7
Da (Khunsa)	1	'Ya (khunsa)	1	5
	(2)		(3)	(12)

Misali na biyu (2)

Mace ce ta mutu ta bar Miji (1/2) da Uwa (1/3) da Baffa khunsa. Nuna rabon gadon a cikin tebur.

Amsa

Wannan rabo an takaice shi a tebur na 4(2) da ke kasa. Ka yi nazarin teburin ta hanyar bin ka'idojin rabo tare da nazarin yadda aka amsa tambayar misali na daya(1) da ke sama.

Abubuwan lura a wannan rabo sune:

1. Baffa khunsa a matsayin namiji zai ci gado da asibci (AS). A matsayinsa na mace ya zama Goggo, amma Goggo Zata'arham ce saboda haka ba za ta ci gado ba domin akwai masu ci da farali, wato ta zama mah-rumah (mrm).

A irin wannan hali khunsa ya kan ci gado a kaddarawarsa ta namiji kawai:

Kashin khunsa = NMJ/2

2. A bangaren kaddarawar khunsa mace Uwa za ta ci gado farlan-wa-raddan. Ka tuna ba a yin raddi ga miji ko matar aure

Mas'alar rabo ita ce mukamin rabon Miji wato biyu (2).

Tebur na 4(2)

Kaddarawar Kaddarawar

Khunsa namiji Khunsa mace

		2			6	Jami'a
		(6)			(2)	(12)
Miji	½	3	Miji	½	1	6
Uwa	1/3	2	Uwa	1/3	1	5
Baffa (kunsa)	As	1	Goggo	Mrm	0	1
		(6)			(2)	(12)

Farlan-wa-raddan

Tambaya ta 4(1)

Mace ce ta mutu ta bar miji (1/2) da shakikiya (1/2) da li'abbi khunsa. Nuna rabon gadon a tebur.

Tambaya ta 4(2)

Mutum ne ya mutu ya bar Uwa (1/3) da li'ummi khunsa. Nuna rabon gadon a tebur? Duba amsoshin a karshen littafi.

YADDA AKE RABA GADO TARE DA MATA-MAZA BISA KARANTARWAR IMAM SHAFI'I

A wannan makaranta ma akan buga rabo a cikin tebura biyu; tebur na farko akan kaddarawar khunsa namiji, tebur na biyu akan kaddarawar khunsa mace.

Bayan haka, Maz-habar Imam Shafi'i sai ta yi nuni akan cewa kowanne magaji za a ba shi kashi "***mafi karanci wanda ya ke tabbas***''. Ma'ana, a kan baiwa kowanne magaji kashin da yafi kankanta daga cikin abinda ya samu a teburan nan guda biyu. Misali, idan kashin da ya samu a kaddarawarsa khunsa namiji shi yafi kankanta, to wannan kashin za a ba shi a karkashin Jami'a. Haka kuma da ace kashin da ya samu a kaddarawarsa khunsa mace ya fi kankanta, to shi za a ba shi a karkashin Jami'a.

Hakika kashi mafi karanci shi ya fi zama tabbas, domin shine kashin da magaji zai iya samu a kowanne irin hali aka tantance shi; namiji ko mace.

Bayan an baiwa kowanne magaji ***kashi mafi karanci wanda ya ke tabbas*** to akan sami shauran dukiya wacce ba a raba ba. To anan sai a ajiye wannan shauran dukiya (a matsayin wakafi) har ya zuwa faruwar daya daga cikin al'amuran nan guda uku (3):

i. Ko dai ya zuwa lokacin da za a iya tantance khunsa namiji ne ko mace ce.

   Anan sai a mika wannan wakafi ga duk wanda ya cancanta tsakanin shi khunsa ko abokan rabonsa.

ii. Ko kuma idan tantancewar ta dauki tsawon lokaci, to sai hukuma ta yi sulhu akan yadda za a raba wakafin ga khunsa da abokan rabonsa.

iii. Ko kuma har idan khunsa ya mutu, to sai a bada iya kashinsa na wakafi ga magadansa.

Duba ka'idojin rabo guda shida (6) da ke kasa tare da misali:

KA'IDOJI

1. Gudanar da rabon a tebura biyu; wato akan kaddarawar khunsa namiji sannan akan kaddarawar khunsa mace. Sai ka inganta mas'alolin guda biyu.
2. Auna tsakanin mas'alolin biyu sai ka lura ko sun yi Tabayuni ko Tawafuki.
3. Nemo mahadar rabon biyu (Jami'a)

a. Idan akwai tabayuni

Za ka buga asalin mas'alar farko cikin mas'ala ta biyu. Duk abinda ka samu shine mas'alar Jami'a.

b. Idan akwai tawafuki

Za ka buga wafkin mas'alar farko cikin mas'ala ta biyu. Duk abinda ka samu shine Jami'a.

4. Nemo Juzu'us sahami

Wato lambar da za ka rubuta a saman asalin mas'ala wacce ake bugawa cikin abinda ke hannun kowane magaji don samun kashinsa a wannan kaddarawar.

Juz'i = Jami'a/Asalin mas'ala

5. Nemo kashin kowanne magaji

Za ka nemo kashin kowanne magaji a teburan nan guda biyu sannan ka auna tsakaninsu, duk wanda yafi kankanta shine kashin wannan magaji ***"mafi karanci wanda ya ke tabbas".***

Rubuta wannan kashi a karkashin Jami'a daura da wannan magaji.

6. Nemo kashin da za'a ajiye (wakafi)

FOMULA 1

Kashin da za a ajiye ga magajin da aka ambata shine;

wakafin = kashinsa (NMJ) - kashinsa (MC)

(magaji)

FOMULA 2

Jumular wakafin dukkan magada, shine;

Jumlar Wakafi = Jami'a - Jumlar kashin magada

MISALI

Mace ce ta mutu ta bar Miji (1/2) da Uwa (1/3) da Dan-uwa shakiki khunsa. Nuna wannan rabo a tebur ka baiwa kowanne magaji kashi ***mafi karanci wanda yake tabbas.***

AMSA

Ka bi wannan amsa tare da duba tebur na 4(3) daga lokaci zuwa lokaci.

- **Gudanar da rabon a tebura biyu,**

i. Kaddarawar khunsa namiji

Asalin mas'alar ya kama gida shida (6). Miji kashi Uku (3), Uwa kashi biyu (2), Shakiki khunsa kashi daya (1) da asibci.

ii. Kaddarawar khunsa mace

Asalin mas'alar ya kama gida shida (6) wacce za a yi aulunta zuwa gida takwas (8), shakikiya khunsa kashi uku (3), Duba tebur.

- **Auna tsakanin mas'alolin biyu**

Asalin mas'alar farko = 6
Asalin mas'ala ta biyu tare da aulu = 8
Shida (6) da takwas (8) sun yi Tawafuki a cikin karamar lamba biyu (2).
Wafkin shida, shine uku (3) domin 6/2 = 3

- **Nemo Jami'a**

Buga wafkin shida (6), wato uku (3), a cikin Asalin masala ta biyu, wato takwas (8)

3 x 8 = 24

Rubuta ashirin da hudu (24) a matsayin Jami'a

- **Nemo Juzu'us Sahami**

Mas'alar farko (6)

Juzu'i = 24/6 = 4

Rubuta hudu (4) a bisa mas'alar farko, wato akan (6).Duba tebur

Mas'ala ta biyu (8)

Juzu'i = 24/8 = 3

Rubuta uku (3) a bisa mas'ala ta biyu, wato akan (8). Duba tebur.

- **Nemo kashin kowanne Magaji a karkashin Jami'a**

Buga juzu'i a cikin abinda da ke hannun kowane magaji kamar haka:

a) Kashin Miji

A kaddarawar khunsa namiji = 4 x 3 = 12

A kaddarawar khunsa mace = 3 x 3 = 9

Idan ka auna tsakanin goma sha biyu (12) da tara (9); $9 < 12$. Tara (9) ita ce mafi kankanta.

Rubuta tara (9) a karkashin Jami'a daura da gidan miji.

b) Kashin Uwa

A kaddarawar khunsa namiji = 4 x 2 = 8

A kaddarawar khunsa mace = 3 x 2 = 6

Za ka dauki shida (6) a matsayin kashin Uwa domin ita ce mafi kankanta. Rubuta shida a karkashin Jami'a daura da Uwa.

c) Kashin shakiki khunsa

A kaddarawar khunsa namiji = 4 x 1 = 4

A kaddarawar khunsa mace = 3 x 3 = 9

Kashinsa na kaddarawar khunsa namiji, wato (4) shine mafi kankanta. Rubuta hudu (4) a karkashin Jami'a daura da khunsa.

- **Nemo wakafi (ajiya)**

Jumlar kashin magada = 9 + 6 + 4 = 19

Jumlar Wakafi = Jami'a – Jumlar kashi

= 24 – 19

= 5

Za'a ajiye biyar (5) a matsayin wakafi har ya zuwa lokacin da aka tantance halin khunsa. Duba tebur na 4(3)

Tebur na 4(3)

Kaddarawar kaddarawar
Khunsa namiji khunsa mace

		4			3	Jami'a
		Asalin (6)			Asalin ~~(6)~~ (8)	(24)
Miji	½	3	Miji	1/2	3	9
Uwa	1/3	2	Uwa	1/3	2	6
Shakiki (khunsa)	As	1	Shakikiya (khunsa)	1/2	3	4
		(6)			(8)	(19)

Wakafi =5

Tambaya ta 4(3)

Mace ta mutu ta bar Miji (1/2) da Shakikiya (1/2) da Dan'uwa li'abbi khunsa.

Nuna rabon ka baiwa kowanne magaji kashi ***mafi karanci wanda ya ke tabbas***. Duba amsa a karshen littafi.

BABI NA BIYAR (5)

RABON GADO TARE DA DAN-CIKI

AL-HAM-LU

A littafi na daya an kawo sharudan gado guda uku (3) wadanda sai sun cika ake cin gado. Daga cikinsu akwai ***"tabbatar da rayuwar magaji a lokacin da mamacin ya mutu".*** Amma Dan-kciki a cikin cikin Uwarsa babu mai iya tantance hakikanin halin da yake ciki sai dai bayan haifuwarsa. Babban kalu bale shine yadda za a tantance a wane hali za a haife shi.

- Shin rayayye za a haifeshi ko matacce?
- Namiji za a haifa ko mace?
- Da daya za a haifa ko tagwaye?

Sanin hakikanin wadannan sai Allah masanin abinda ke cikin mahaifa. Saboda haka wasu su kan jinkirta rabo har sai bayan haifuwa, a lokacin nan an tantance rayuwar jinjiri kuma an san ko namiji ne ko mace ce.

Amma babu laifi a gaggauta rabo kafin haifuwa. Za a yi rabo na farko a baiwa kowane magaji kashinsa a hannunsa, sai a ajiye kashin Danciki a saurari haifuwa.

Idan an haife shi rayayye sai a ba shi abinda ya cancanci ci na gado. Idan kuwa an haife shi matacce ba zai ci gado ba sai a juyarda kashinsa ga abokan rabonsa.

Sharudan bayar da gado ga Dan-ciki

Dan-ciki zai ci gado ne idan ya cika wadannan sharrruda guda biyu (2):

1. Lallai ne Dan-ciki ya kasance ***samamme a cikin mahaifiyarsa*** a lokacin da wanda zai gada ya mutu. Za'a iya gane hakan musamman ta hanyoyin zamani na awun ciki da 'scanning'.
2. Lallai ne ya kasance an haife shi ***rayayye, rayuwa wacce take tabbatacciya.***

Sharadi na Farko

Dan-ciki ya kan kasance sammame a cikin uwarsa, farko, idan akwai alamomin cikin sannan kuma a ka haife shi a kowanne lokaci ko da bayan shekaru biyu ne daga mutuwar mamacin.

Sayyada Aisha (R.A) ta ce, ***"dan ciki baya zama a cikin uwarsa sama da shekara biyu koda kimanin da kadawar mazari".*** Ma'ana tilas a haife shi ko ayi barinsa.

Amma a Maz-habar Imam Malik Da zai iya zama a cikin mahaifa har tsawon shekaru hudu.

Sharadi Na Biyu

Akan tabbabatar da cewa an haifi Dan-ciki ***"rayayye kuma mai tabbatacciyar rayuwa"*** ta daya daga cikin wadannan hanyoyi:

Ko dai aji ya yi kuka, ko atishawa, ko kuma ya kama nonon uwarsa, ko kuma aga ya yi motsi tsawon lokaci kafin ya mutu.

Yayin da aka tabbatar da rayuwarsa ta wadannan hanyoyi to zai ci gado, haka kuma za a sallaceshi in ya mutu. Amma idan aka haife shi matacce ko da wani sashen jikinsa ne ya fito amma ba a kammala haifuwarsa ba ya mutu, ba zai ci gado ba kuma ba za a sallace shi ba.

A wani Hadisi, rayuwar Nasa'i da Turmuzi, Manzon Allah (S.A.W) ya ce;



Ma'ana, "Idan jinjiri ya yi kuka za a sallace shi kuma zai ci gado"

Dangantakar Dan-ciki da Mamaci

Dangantakar da ke tsakanin Mace mai ciki da Mamaci ta kan nuna irin dangantakar wannan Dan-ciki da Mamacin.

Misali, idan mamaci ya bar matarsa da ciki za ka ga cewa abinda za ta haifa Da ne ko 'Ya ce ga mamacin. Matar Dan-mamaci za ta haifi jika Dan-da ko 'Yar-da ga mamacin. Duba tebur da ke kasa ya dunkule irin wadannan dangantaka:

Tebur mai nuna dangantakar Dan-ciki da Mamaci

S/N	MAI CIKI	ABINDA ZA TA HAIFA	KO ZAI CI GADO	
			NAMIJI	MACE
1.	Matar mamaci	Da ko 'Ya	✓	✓
2.	Matar Dan-mamaci	Dan-da ko 'Yar-da	✓	✓
3.	Matar Jikan-mamaci	Dan-jika ko 'Yar-jika	✓	✓
4.	Uwar mamaci (a gidan ubansa)	Shakiki ko shakikiya	✓	✓
5.	Matar Uban Mamaci (Yaduko)	Li'abbi ko li'abbiya	✓	✓
6.	Uwar mamaci (a gidan wani mijink)	Li'ummi ko li'ummiya	✓	✓
7.	Matar shakiki ga mamacin	Dan shakiki ko 'Yar shakiki	✓	X
8.	Matar li'abbi ga mamacin	Dan-li'abbi ko 'Yar-li'abbi	✓	X
9.	Matar Baffa Shakiki	Dan baffa shakiki ko 'Yar baffa shakiki	✓	X
10.	Matar Baffa Li'abbi	Dan baffa li'abbi ko 'Yar baffa li'abbi	✓	X
11.	'Yar Mamaci	Dan-'ya ko 'Yar-'ya	X	X
12.	Shakikiya ga amamaci	Dan-shakky ko 'Yar-shakky	X	X

Yadda Ake Raba Gado Tare Da Dan-ciki

Idan akwai Dan-ciki a cikin magada za a gudanar da rabo a cikin tebura guda biyu (kamar dai khunsa). Tebur na farko akan kaddarawar Dan-ciki namiji ne, tebur na biyu akan kaddarawarsa mace. Za a baiwa kowanne magaji kashi ***mafi karanci wanda ya ke tabbas*** (kamar dai khunsa). Za a ajiye wakafi har ya zuwa haifuwar jariri.

Dan-ciki ya na da halaye biyar (5) na cin gado:

1) <u>A inda Dan-ciki ya kadaita ko kuma ya kare abokan rabonsa</u>

Ka'ida anan ita ce za a ajiye duk dukiyar gaba daya har ya zuwa haifuwa. Idan an haife shi rayayye sai a bashi duka dukiyar a hannunsa. Amma idan aka haife shi matacce sai a juyar da dukiyar ga wadanda suka cancanta daga cikin abokan rabo wadanda ya kare a da can.

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Matar Dansa mai ciki da Dan-uwa li'ummi.

A wannan misali Dan-ciki ya kare li'ummi domin Dan-cikin reshe ne ga mamacin. Idan an haife shi namiji ya zama Dan-da , saboda haka zai ci dukiya gaba dayanta da asibci. Idan an haife shi mace ya zama 'Yar da, za ta ci dukiya gaba daya, rabi faralan sannan rabi raddan. Nuna rabon a tebur.

2) <u>A inda Dan-ciki ba ya cin gado ta kowacce fuska</u>

Wato ba ya cin gado walau a kaddarawarsa namiji ko a kaddarawarsa mace.

KA'IDA

Anan ba za a yi la'akkari da wannan Dan-ciki ba domin ba shi da gado ta kowacce fuska. Sai a raba dukiya ga sauran magada.

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da Uba kuma Uwarsa mai ciki wacce ta ke aure a gidan wani miji ba Uban mamaci ba.

Amsa anan ita ce, za a raba dukiya ga Matar aure da Uba da Uwa su kadai, domin ko da an haife shi zai zama li'ummi ko li'ummiya.

Uba ya kare li'ummai daga cin gado saboda haka babu gado ga wannan Dan-ciki ta kowacce fuska. Nuna rabo.

3) <u>A inda Dan-ciki zai ci gado ta fuska daya kawai</u>

Wato zai iya cin gado ta kaddarawarsa namiji kawai (ko akasin haka).

KA'IDA

Za a gudanar da rabo a bisa kaddarawar Dan-cikin zai ci gado, sannan a baiwa kowanne magaji kashinsa. Sai a ajiye kashin Dan-cikin har ya zuwa haifuwa. Idan ya tabbata magaji sai a bashi kashinsa. Idan kuwa ba zai ci gado ba sai a juyar da kashin nasa ga abokan rabo.

A nan za ka tara jumlar kashin da ke hannun abokan rabo ka sanya ta Jami'a wacce za ta dunkule rabon.

<u>Misali</u>

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da Baffa da kuma Matar shakikinsa mai ciki.

<u>Amsa</u>

Za a baiwa Matar aure rubu'i (1/4) , sai a ajiye shauran kashi uku cikin hudu (3/4) har ya zuwa bayan haifuwa. Idan an haife shi namiji ya zama Dan shakiki sai a bashi abinda aka ajiye, domin ya kare Baffa.

Idan an haife shi mace ya zama 'Yar shakiki ba za ta ci gado ba, domin ta na cikin zul-arham kuma akwai masu cin gado da farali. Anan Baffa zai ci abinda aka ajiye da asibci. Nuna rabon a tebur?

4) <u>A inda Dan-ciki zai ci gado sannan kashinsa ksun daidaita a fuskokin biyu</u>

Wato kashinsa na kaddarawar namiji yayi daidai da kashinsa na kaddarawarsa mace.

KA'IDA

Za a gudanar da rabo a baiwa kowanne magaji kashi cikakke, sannan a ajiye kashin Dan-ciki har ya zuwa haifuwa. Idan an haife shi rayayye mai

tabbatacciyar rayuwa sai a ba shi kashinsa. Amma idan an haife shi matacce sai a juyar da kashinsa ga abokan rabo.

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Shakikiya da Li'abbiya da Uwa mai ciki wacce ta ke auren Miji ba Uban mamaci ba.

Amsa

Dan-ciki, kowane irin jinsi aka haifa, namiji ko mace, rabonsa ya kama sudusin dukiya yadda ya ke a tebur na 5(1).

Za a ajiye kashin li'ammi har ya zuwa haifuwa. Idan an haife shi rayyayye sai a bashi wannan kashi. Idan kuwa an haife shi matacce sai a juyar da kashinsa ga abokan rabo.

Tebur na 5(1)

Kaddarawar			Kaddarawar			
Dan-ciki namiji			Dan-ciki mace			
						Jami'a
		(6)			(6)	(6)
Shakikiya	1/2	3	shakikiya	1/2	3	3
Li'abbiya	1/6	1	Li'abbiya	1/6	1	1
Uwa	1/6	1	Uwa	1/6	1	1
Li'ummi (Dan-ciki)	1/6	1	Li'ummiya ('Yar-ciki)	1/6	1	0
		(6)			(6)	(5)
						Wakafin 1

5. A inda Dan-ciki zai ci gado amma kashinsa sun banbanta a fuskokin biyu

KA'IDA

Za a buga rabo a cikin tebura biyu, farko a kaddarawar Dan-ciki namiji, sannan a kaddarawarsa mace. Za a baiwa kowanne magaji ***kashi mafi karanci daga cikin abinda ya samu a bangarorin biyu.*** Sai a ajiyewa Dan-ciki kashi wanda yafi girma a tsakanin abinda ya samu a teburan biyu. Idan an haife shi rayayye sai a bashi abinda ya cancanci ci daga ciki abinda aka ajiye masa.

Idan ya cancanci dukkan abinda aka ajiye sai a bashi. Idan ya ci sashe kawai, to za a bada sauran ga abokan rabon su hada akan nasu.

Wakafi = Jami'a - Jumlar kashin magada.

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Matarsa mai ciki da Uba da kuma Uwa. Nuna rabon a tebur?

Tebur na 5(2)

Kaddarawar Dan-ciki namiji — Kaddarawar Dan-ciki mace

					Jami'a	
		(24)			(24)	(24)
Matar aure	1/8	3	Matar aure	1/8	3	3
Uwa	1/6	4	Uwa	1/6	4	4
Uba	1/6	4	Uba	As, 1/6	5	4
Da (a ciki)	As	13	'Ya (a ciki)	1/2	12	12
		(24)			(24)	(23)

Wakafin 1

BABI NA SHIDA (6)

RABON GADO TARE DA WANDA YA ‘BACE

AL-MAF-KUD

AL-MAF-KUD shi ne wanda ya ‘bace, ba a san inda ya ke ba, kuma ba a jin ko labarinsa, ballantana a san a halin da ya ke ciki. Shin ya na halin rayuwa ne ko kuwa ya mutu !

Sharadi ne ba za a zartadda duk wata mu’amalla da ta shafi wanda ya bace ba har sai an tabbatar da halin da ya ke ciki. Ma’ana ba za a gudanar da su ba har sai an tantance ko yana halin rayuwa ko kuma ya mutu. Misalai a nan su ne;

1. Matarsa ba za ta yi Idda ta yi aure ba har sai an tantance ya mutu.
2. Ba za a raba dukiyarsa gado ba har sai an tantance ya mutu
3. Ba zai ci gadon dukiya ba har sai an tantance ya na da rai a lokacin da mamacin ya mutu.

Yadda ake tantance halin wanda ya ‘bace

Ana tantance halin wanda ya ‘bace ta wadannan hanyoyi guda uku (3):-

1. Ko dai a sami sahihin labarin cewa ya na da rai ko bayyanarsa shi kansa
2. Ko kuma a sami sahihin labarin mutuwarsa ko ganin gawarsa.
3. ko kuma dai ‘bacewar ta sa ta dauki tsahon lokaci wanda Alkali zai iya tabbatar da hukunci akan cewa ya mutu (abinda ake cewa Gaiba)

Malaman fiqhu sun yi sabani akan yadda za a tabbatar da mutuwar wanda ya ‘bace. (Duba littafin Al-mawarith fish’shari’atil islami na sheikh Muhammad Aliyu As-sabuni)

Mafi rinjayen zance shine akan fawwala lamarin ***al-maf-kud*** a hannun Alkali. Alkali zai yi nazari ya yanke hukuncin da ya dace. Farko, Alkali zai yi duba ga irin halin da ***al-maf-kud*** din ya ‘bace a cikinsa.

A. <u>Idan al-muf-kud din ya ‘bace a halin da ake karfafa zaton halakarsa</u>

Kamar ya ‘bace a filin yaki, ko a cikin girgizar kasa, ko a jirgin ruwa wasu suka nutso wasu suka tsira, ko surkukin daji mai yawan ‘yam-fashi da namun daji da dai sauransu. Hukunci anan shine za a yi ta nemansa har shekara hudu (4).

Idan ba a same shi ba kuma ba a ji labarinsa ba har zuwa shekara hudu (4), to Alkali zai iya tabbatar da mutuwarsa. Daga nan za a iya raba dukiyarsa gado, kuma matarsa za ta iya yin Iddar mutuwa sannan ta yi aure.

B. <u>Idan *Al-maf-kud* ya ‘bace a halin da ba a karfafa zaton halakarsa</u>

kamar ya yi balaguro, ko tafiyar neman ilimi, ko ya tafi fatauci da sauransu. Hukunci a nan sai a yi ta nemansa tsawon shekaru masu tarin yawa. Za a lura da mutuwar tsarekunsa a cikin garinsu, domin mutuwarsu alama ce mai nuna cewa shima babu mamaki ya mutu. Ana iya fahimtar haka lokacin da aka lura shakarunsa na haifuwa sun kai casa’in (90). Amma Imam Malik ya rawaito shekara saba’in (70) da haifuwa daga Hadisin Manzon Allah (S.A.W)


الحديث المشهور: (أعمارَ أمتى ما بين الستين والسبعين

<u>Ma’ana</u>

Manzon Allah (S.A.W) ya ce, ‘‘tsawon rayuwar (mutane) a cikin al’ummata tsakanin shekara sittin (60) zuwa saba’in (70)‘‘.

Bayan tabbatar da wannan hukunci za a iya raba dukiyarsa gado haka kuma matarsa za ta yi Iddar mutuwa sannan ta yi aure.

YADDA AKE RABA GADO TARE DA AL-MAF-KUD

Wanda ya ‘bace zai ci gado idan har an tabbatar da rayuwarsa a lokacin da mamacin ya mutu. Amma ba zai ci gado ba idan an tabbatar da mutuwarsa ko kuma Alkali ya zartadda hukunci akan cewa ya mutu.

AL-MAF-KUD ya na da halaye guda biyu (2) na cin gado;-

(1) A inda ya kadaita ko kuma ya kare abokan rabaonsa daga cin gado

Ka’ida

Za a ajiye dukiya gaba dayanta har sai an tabbatar da halin al-maf-kud.

Idan an tabbatar da rayuwarsa sai a ba shi dukiya gaba daya. Amma idan Alkali ya tabbatar da mutuwarsa sai a raba dukiyarsa ga sauran abokan rabonsa.

Misali

Mutum ne ya mutu ya bar Shakiki da Shakikiya da kuma Da wanda ya ‘bace. Bayyana rabon.

Da ya kare duk ‘Yan’uwa daga cin gado, saboda haka za a ajiye dukiyar har sai an tabbatar da halin da wannan Da yake ciki.

2. A inda zai ci gado tare da abokan rabo

KA’IDA

Za a gudanar da rabo akan kaddarawa biyu (2). Farko, akan kaddarawarsa rayayye, na biyu akan kaddarawarsa matacce. Za a ajiye kashin wanda ya ‘bace har ya zuwa bayyanar halinsa. Sannan za a baiwa kowanne magaji kashinsa kamar haka;-

i. **Kashi cikakke,** idan har Al-maf-kud ya ci gado a kaddarawar biyu sannan kashin nasa a bangarorin biyu sun zama daidai.
ii. **Kashi mafi kankanta**, idan Al-maf-kud yaci gado a kaddarawar biyu amma kashinsa sun banbanta a bangarorin biyu.
iii. **Ba za’a bashi komai ba a rabon farko**, idan ya ci gadon a kaddarawa daya kawai (bangare daya kawai)

MISALAI:

Misali na daya (1)

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da Uwa da Li'abbi da kuma Shakiki wanda ya 'bace. Nuna rabon?

AMSA An dunkule rabon a tebur na 6 (1)

Tebur na 6 (1)

Kaddarawarsa Rayayye Kaddarawarsa Matacce

		(12)			(12)	(12)	
Matar Aure	¼	3	Matar Aure	1/4	3	3	
Uwa	1/6	2	Uwa	1/3	4	2	WKF 2
Li'abbi	MJB	0	Li'abbi	AS	5	0	WKF 5
Shakiki (Maf-kud)	AS	7	Shakiki (Maf-kud)	MRM	0	0	WKF 7
		12			(12)	(5)	

Karin bayani akan tebur na 6 (1)

Tebur na 6 (1) ya nuna rabon farko kafin a tantance halin Al-maf-kud. Za'a baiwa kowanne magaji kashinsa da ke karkashin Jami'a.

Amma bayan tantance halin Maf-kud za a kammala rabon kamar haka:

- Idan ya bayyana rayayye za a bada wannan wakafin (7) da ke ajiye ga Al-maf-kud din, rabo ya kamala.
- Idan kuma aka zartadda hukunci ya mutu ,to, za a raba wakafin (7) din ga abokan rabo kamar haka:

Uwa za a ba ta Karin kashi = 2

Li'abbi za a bashi kashi = 5

Jumulla an rabe wannan wakafi kashi = 7

Misali na biyu (2)

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da Li'ummi da Dan-baffa shakiki da kuma 'Yar -da wacce ta 'bace. Nuna rabon a tebur.

AMSA

TEBUR NA 6 (2)

Kaddarawarta Rayayyiya Kaddarawarta Matacciya

3 2 Jami'a

		(8)			(12)	(24)	
Matar Aure	1/8	1	Matar Aure	¼	3	3	WKF 3
Li'ummi	MJB	0	Li'ummi	1/6	2	0	WKF 4
Dan baffa shakiki	AS	3	Dan baffa shakiki	AS	7	9	WKF 5
"Yar-da (Mafkuda)	1/2	4	"Yar-da (Mafkuda)	MRM	0	0	WKF 12
		(8)			(12)	(12)	

Karin bayani akan tebur na 6 (2)

Tebur na 6 (2) ya nuna rabon farko kafin a tantance halin Al-maf-kuda. Za a baiwa kowanne magaji kashinsa da ke karkashin Jami'a.

Amma bayan tantance halin Maf-kuda za a kammala rabon kamar haka:

- Idan ta tabbata rayayyiya za a ba ta wakafin (12), wato rabo ya kamala ke nan.
- Amma idan an zartad da hukunci cewa ta mutu za a raba wakafi a karawa abokan rabo kamar haka:

Matar aure karin kashi = 3

Li'ammi karin kashi =4

Dan baffa shakiki karin Kashi = 5

Jumulla an rabe wakafin da aka ajiye = 12

Tambaya ta 6 (1)

Mutum ne ya mutu ya bar Matar aure da Uwa da Shakiki da kuma Dan-da wanda ya 'bace, nuna rabon a tebur. Sai ka duba amsa a karshen littafi.

BABI NA BAKWAI (7)

GADON MAGADA JUNA WADANDA SU KA MUTU TARE

Ka duba irin hadurran da Dan-Adam ke fuskanta a kullum hudowar rana daga gabas ya zuwa faduwarta a yamma. Rayuwar ke nan dai wata rana ayi kuka wata rana ayi dariya. Babu abinda mutum zai yi sai hakuri da kuma sallamawa ga ikon Mahallicci Maijuya al'amurran bayinSa.

Sau da yawa ''Yan'uwa magada juna su kan halaka a cikin wata musiba yadda ba za a iya tantance wanda ya riga mutuwa ba a tsakanin su. Misali, a wasu lokutan yana da wahala a fahimci wanda ya riga mutuwa a cikin jirgin sama ko jirgin ruwa daya kife ko ya nutso a cikin teku ko mutanen da suka mutu a cikin teku ko hadarin mota da sauransu. Tambayoyi biyu a nan su ne :

1. Wane sharadi ne sai ya cika kafin wadannan halakakku su ci gadon junansu?
2. Kuma yaya za ka raba gado idan irin wannan mush-kila ta faru?

KA'IDOJI

1. Sharadi ne kafin a raba gado *"a tabbatar da rayuwar magaji a lokacin da wanda za a gada din ya mutu".* Saboda haka matukar an fahimci wanda ya riga mutuwa daga cikin 'Yan'uwa magada juna to al'amari ya bayyana a fili. Magajin da aka tabbatar da rayuwarsa zuwa wani lokaci, komai kankantar lokacin zai ci gadon wannan da ya riga shi mutuwa. Domin idan ka duba za ka ga sharadi ya cika, wato "an tabbatar da rayuwar magaji bayan mutuwar wanda za'a gada".

   Misali, mota ce ta yi hadari da 'yan'uwa su biyu sai Dan'uwa na farko ya mutu anan take amma na biyu bai mutu ba sai bayan misalin awa daya (ko kasa a haka) ka ga wannan Dan'uwa na biyu zai ci gadon na farko, sannan kuma sai a raba dukiyar mamaci na biyun ga magadansa.
2. Amma idan 'Yan'uwa magada juna suka halaka sannan ba a tantance wanda ya riga mutuwa ba, to babu gado a tsakaninsu, wato babu

wanda zai ci gadon wani a tsakaninsu. Akan raba dukiyar kowannensu ga nasa magadan kawai.

MISALI

Mutum ne da matarsa su ka mutu a cikin wata musiba yadda ba a tantance wanda ya riga mutuwa ba. Dukkaninsu su biyu suna da dukiya kuma tsakaninsu akwai 'Ya'ya Maza su uku. Bayan haka Matar ta na da Da tare da wani mijin. Sannan kuma shi wannan Miji mamaci ya na da wata Matar aure wacce su ka haifi Da tare da ita. Raba wannan gado?

AMSA

Tantance Magadan Kowanne Mamaci



Magadan Kowanne Mamaci

Miji (marigayi) **Matar Aure (marigayiya)**

1. **Matar Aure**
2. **Da** | **Li'abbai**
3. **Da (3)**

1. **Da (3)**
2. **Da** | **Li'ummai**

Tebur na 7 (1)

		(8)	(32)
Matar Aure	1/8	1	4
Da (4)	AS	7	7x4
		(8)	(32)

Tebur na 7 (2)

		(4)	
Da (4)	AS	1x4	
		(4)	

AMSOSHIN TAMBAYOYI

Amsar Tambaya Ta 1 (1)

(1) (1) Jami'a

		(24)			(12)	(24)
Matar aure	1/8	3				3
Uba	1/6 ,As	5				5
Uwa	1/6	4				4
'Yar-da	½	12	TMT			0
		(24)	Miji	¼	3	3
			Uwa	1/6	2	2
			'Ya'ya maza (2)	AS	4	4
			'Ya'ya mata (3)		3	3
					(12)	(24)

- Auna (12) da (12)-Tamasul
- Jami'a=24
- Kowace 'Ya kashi daya (1) -Kowane Da kashi biyu (2)

Amsar Tambaya Ta 1 (2)

(5) (3) (5) Jami'a

		(24) (27)	(135)			(12)	(405)
Uwa	1/6	4	20				60
Uba	1/6	4	20	YMT		0	0
Matar aure	1/8	3	15				45
'Ya'ya mata (5)	2/3	16	80				240
		(27)	(135)	Matar Aure	1/4	3	15
				Shakikiya	1/2	6	30
				Li'ummi	1/6	2	10
				Dan-dan'uwa Shakiki	AS	1	5
						(12)	(405)

<u>Auna 20 da 12 - Tawafuk</u>

i. Wafkin $20 = \frac{20}{4} = 5$

ii. Wafkin $12 = \frac{20}{4} = 3$

iii. Jami'a $= 3X135 = 405$

iv. Kowace 'Ya mace ta na da , $240/5 = 48$

Amsar Tambaya Ta 1 (3)

(13) ***(3)***

		(~~12~~) (15)			(~~12~~) (13)	(195)
Miji	¼	3	YMT			0
‘Ya’ya mata(2	2/3	8				104
Uwa	1/6	2				26
Uba	1/6	2				26
		(15)	Shakikiya	½	6	18
			Uwa	1/6	2	6
			Matar aure	¼	3	9
			Li’ummi	1/6	2	6
					(13)	(195)

- Auna (13) da (3) - Tabayun

-Jami’a $= 13X5 = 195$ Kowace ‘Ya ta na da $= \ 104/2 = 52$

Amsar Tambaya Ta 4 (1)

Kaddarawar Khunsa Namiji **Kaddarawar Khunsa Mace**

14 **4 Jami'a**

		(2)			~~(6)~~ (7)	(28)
Miji	½	1	Miji	1/2	3	13
Shakikiya	½	1	Shakikiya	1/2	3	13
Li'abbi (Khunsa)	AS	0	Li'abbiya (Khunsa)	1/6	1	2
		(2)			(7)	(28)

Anyi aulu ga li'abbiya khunsa

Amsar Tambayar ta 4 (2)

Kaddarawar Khunsa Namiji **Kaddarawar Khunsa Mace**

1 **1**

Jami'a

		~~(6)~~ (3)			~~(6)~~ (3)	(3)
Uwa	1/3	2	Uwa	1/3	2	2
Li'ummi (Khunsa)	1/6	1	Li'ummiya (Khunsa)	1/6	1	1
		(3)			(3)	(3)

Farlan-wa-raddan.

<u>Amsar tambaya ta 4(3)</u>

Kaddarawar Khunsa namiji ***kaddarawar khunsa mace***

7 2 Jami‘a

		(2)			(6) (7)	(14)	
Miji	½	1	Miji	½	3	6	WKF 1
Shakky	½	1	Shakky	½	3	6	WKF 1
Li’abbi(khunsa)	AS	0	Li’abbiya(khunsa)	1/6	1	0	
		(2)			(7)	(12)	WKF 2

An yi aulu ga li‘abbiyya.

Amsar Tambaya ta 6(1)

Kaddarawarsa Rayayye **Kaddarawarsa Matacce**

1 **2** **Jami‘a**

		(24)			(12)	(24)	
Matar aure	1/8	3	Matar aure	1/4	3	3	WKF=3
Uwa	1/6	4	Uwa	1/3	4	4	WKF=4
Shakiki	MJB	0	Shakiki	AS	5	0	WKF=10
Dan-da (Maf-kud)	As	17	Dan-da (Maf-kud)	Mrm	0	0	Jumlar WKF=17
		(24)			(12)	(7)	

LITTAFFAN DA AKA DUBA

1) Tarjamar Ma’anonin Al-ƙur’ani Mai Girma – na Sheikh Abubakar Mahmud Gumi. (1979)
2) Al-mawarith fish-shari’atil islami - na Sheikh Muhammad Aliyu As-sabuni (2002)
3) As-halul Madariki – (Juz’i na uku) – Sarhin Sheikh Abubakar Kash-nawi akan Ir-shadus Salik na Ibn As-kar. Bugun Madaba’ar Dar El-fikr, Beirut-Lebanon. (2000)
4) Min-hajul Muslim – (Sabon bugu) na Sheikh Abubakar Jabir Al-jaza’iri; Bugun Madaba’ar Dar El-fikr, Beirut – Lebanon. (2003)
5) Muwadda Imam Malik – ruwayar Yah-ya dan Yah-ya Al-laisi; Bugun Madaba’ar Dar El Kutubul Ilmiyi, Beirut-Lebanon (1984)